## DARASI NA 44: KARATUN GAJERUN LABARAI

Kande ta tafi asibiti domin a duba lafiyarta. Kande, yarinya ce mai tsafta. Ko lokacin da za ta tafi asibiti ta saka wankakkun kayayyaki.

Lokacin da Kande ta isa asibiti, an bata kujera ta zauna domin ta jira likita. Da likitan ya zo ya duba ta, sai ya rubuta mata maganin ciwon kai da suka haɗa da ƙwayoyi da kuma na ruwa sannan ya bata shawarar cewa ta riƙa wanke haƙoranta sosai da abin goge baki.

Da Kande ta koma gida, sai ta bai wa mahaifiyarta labarin yadda aka bata kujera ta zauna tare da cewa ta ga irin kujerar da kafinta yake ƙerawa a asibiti. Sai mahaifiyarta ta ce da ita ai likitanci da kafitanci duk sana'o'i ne da ake samun horon yin su a manyan makarantu. Sannan ta ƙara da cewa, ina yi miki fatan ki samu nasarar cin jarabawarki ta sikandire domin kema ki je ki karanto ɗaya daga ciki, domin ki zama mai bayar da gudunmawa a cikin al'umma. Ina roƙon Allah Ya yaye miki wannan cuta Ya kuma saka ta zama kaffara a gare ki.